# MU GUJI YIN HASSADA

## WASIKA ZUWA GA MUSULMI DAGA WAZIRIN KATSINA A KAN ILLOLIN HASSADA DAGA AYOYIN AL-KUR'ANI DA HADISSAI

Na
**WAZIRIN KATSINA Na 5**
**Prof. Sani Abubakar Lugga,** MFR

**By:**
**Professor Sani Abubakar Lugga, MFR**
**The 5th Waziri of Katsina**
**Professor of Management Studies**
**Doctor of Philosophy in Conflict Management**
**Fellow of the Nigerian Institute of Management**
**Fellow of the Institute of Management Consultants (Nigeria)**
**Fellow of the Institute of Professional Financial Managers (UK)**
**Fellow of the London Graduate School, London, United Kingdom**
**Key Founder and former Senior Lecturer, Al-Qalam University, Katsina**
**Visiting Prof., Ecole Superieure Universitaire, Cotonou, Benin Republic**
**Visiting Professor at St. Clements Private Swiss University, Switzerland**
**Committee Member, Nigeria Supreme Council for Islamic Affairs**
**Committee Chairman, Jama'atuNasril Islam, Kaduna, Nigeria**
**Member of Sultan Foundation for Peace and Development**
**Executive Member, Interfaith Initiative for Peace, Nigeria**
**Ambassador of Universal Peace Federation, New York**
**Member of Professors World Peace Academy, Korea**

**www.books.luggaweb.com**

**Haƙƙin Mallaka © Prof. Sani Abubakar Lugga**
**© Copyright: Prof. Sani Abubakar Lugga**

**Ɗab'in Maɗaba'ar Lugga**
**Gidan Lugga, Titin Kofar Marusa, Katsina,**
**Jihar Katsina, Najeriya.**

**An Fara Wallafawa Da Bugawa:**
**Jimada Thani 1426 Hijra (July 2005)**

**An Sake Bugawa:**
**Muharram 1443 Hijra (August 2021)**

بسم الله الرحمن الرحيم.
نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي
رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين.

*Zuwa ga 'Yan Uwana Musulmi,*

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinƙai. Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Maɗaukaki wanda muke gode mawa domin ni'imomin da ya yi mana. Tsira da Amincin Allah sun tabbata ga Manzon Allah, Annabi Muhammadu, da Alayensa da Sahabbansa.

Assalamu Alaikum,

Na yi wannan wasiƙa ce ga dukkan 'yan-uwa Musulmi domin halin da muke ciki a yau, na yawan yi wa juna hassada. Ni, a gani na, Hassada ita ce tushen rashin hada kawunan mu a Najeriya har ta kai mu ga cewa a yau Musulmi na cikin halin ƙaƙa-nika-yi. Yau da za mu kauda hassada ga juna, mu riƙe igiyar Allah kamar yadda Allah Ya bayyana mana a cikin Al-Qur'ani kuma Annabi Muhammadu (SAW) ya koya mana, to da sauran abokan zaman mu sun yi sha'awar mu da girmama mu. Kuma wannan koyi da Manzon Allah (SAW) shi zai sa waɗanda ba Musulmi ba su fahimci cewa tushen zaman lafiya dai shine Musulunci.

Ya 'yan-uwa Musulmi, ya kamata mu koma ga abinda addinin mu na Musulunci yace mu yi wa juna wanda kuma shine iyayen mu da kakannin mu suka riƙa har suka zama

zakaru a wannan Kasa tamu ta Najeriya. Duk ɗan shekara hamsin da fiye da haka, ya san cewa iyayen mu da kakannin mu halayyar “gasa” suka riƙa yi da juna harta kai ga cewa ko wannen su ya yi zara. Amma yanzu batacciyar “gaba” muke yi da juna shi ya sa ko wannen mu ya faɗi kasa har wasu suka hau bisa kawunan mu. Kuma abin takaici shine, sai muka koma gefe guda muna zargin cewa an danne Musulmi al-hali kuwa mu muka jawo ma kawunan mu abin da ke faruwa musamman ta yi ma juna hassada wadda ita ce taba wasu halin danne mu.

Wasiƙa kamar wannan ba zata yiwu ba ga Al-Majiri kamar ni, sai da gudummuwa daga Malamai. Don haka nike mika godiya ta ga Malamaina wadanda suka duba wannan wasiƙa kuma suka bada shawarwari da kuma waɗanda ni kan nemi ilmi wajensu. Malaman sun haɗa da Liman Abba Muhammad Aliyu, Sheik Abubakar Ibrahim Charanci, Ustaz Labaran Imam Saulawa da Ustaz Muhammad Sagir Adam. Muna bukatar duk wanda ya ga kuskure a wannan wasika to don Allah ya gyara kuma ya aiko mana domin mu ma mu gyara.

Muna roƙon Allah (SWT) Ya sanya albarka ga wannan aiki, Ya yi mana gafarar kura-kuran mu kuma Ya sanya mu cika da imani idan ajalin mu ya zo, ameen.

## Muƙaddima

Hassada dai wata kalma ce wadda ana iya yi mata fassara da dama kuma tana da ginshiƙai da dama don haka yana

da wuya a fitar da fassarar ta guda ɗaya. Amma ana iya kokarin bayyana hassada kamar haka:-

1. Yin baƙin ciki ko ganin ƙyashi da wani abu ko wata ni’ima da Allah (SWT) Ya ba wani kamar yadda Allah (SWT) Ya ke cewa:

أَمْ يَحْسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۖ

“*Ko kuwa suna yi ma mutane* ***hassada*** *ne bisa ga abinda Allah Ya basu daga falalarsa?”* (Suratun Nisaa: 54)

2. Yin zunde da yawo da gulma a bisa ƙarya don a ɓata sunan wani. Allah (SWT) Ya hana wannan a inda Ya ke cewa:

وَلَا تُطِعْ كُلَّ حَلَّافٍ مَّهِينٍ ﴿١٠﴾ هَمَّازٍ مَّشَّآءٍ بِنَمِيمٍ ﴿١١﴾

*“Ka da ka bi dukkan mai rantsuwa, wulaƙantacce. Mai zunde, mai yawo da gulma*” (Suratul Qalam: 10-11)

3. Yin munafunci, watau a fili kana tare da mutum amma a zuciya baka tare da shi kuma kana ta ƙarya domin ka bata shi a bayan idonsa. Allah (SWT) Ya saukar da Sura guda kacokam a cikin Al-Qur’ani domin munafukai kuma Ya kira ta da sunan “Suratul Munafiqun”. A cikin aya ta farko (1) ta wannan Sura Allah (SWT) Ya ce:

وَٱللَّهُ يَشْهَدُ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ لَكَٰذِبُونَ

*"... Allah Ya na shaidar lallai munafukai, hakika, maƙaryata ne"* Kuma a aya ta shidda (6) Allah Ya ce ko da Annabi Muhammadu (SAW) zai roƙa ma munafukai gafara, to, ba zai Yi masu gafara ba. Ga ayar:-

سَوَآءٌ عَلَيْهِمْ أَسْتَغْفَرْتَ لَهُمْ أَمْ لَمْ تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ لَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ

*"Duk daya ne ko ka nema masu gafara, ko baka nema masu ba, Allah ba zai yi masu gafara ba".*

4. Yin tone-tonen asirin wani domin keta masa mutunci. Al-Bukhari ya ruwaito a cikin littafinsa kashi na 8, hadisi na 90, cewa Abu Huraira (RLA) ya ce, "Manzon Allah (SAW) yana cewa: *"Ku yi hankali da zargin juna domin zargi shine zancen ƙarya mafi muni, kada ku yi ta neman laifin wasu kuma kada ku yi leƙen asirin juna…….."*

Ana iya cewa abubuwan da aka gina hassada a kai sun hada da baƙin-ciki, gulma, zunɗe, ƙarya, munafunci, ganin ƙyashi, tone-tone na babu gaira babu dalili da dai sauran miyagun ɗabi'u da ayyuka. Watau a taƙaice hassada ita ce ka riƙa jin zafi ko ganin ƙyashin wata falala da Allah (SWT) Ya yi ma wani bawansa kuma yana

amfani da ita kamar yadda Allah Ya ce a yi, kai kuma ka yi ta ƙoƙarin yadda zaka raba shi da ita ko kuma yadda zaka ɓata masa suna.

Ya ‘yan-uwana Musulmi, yana da kyau a fahimci cewa idan Allah (SWT) Ya ba wani wata falala amma yana al-mubazzarantar da ita to wajibi ne a yi masa wa’azi amma ba a tafi ana zunɗen sa ba. Ana iya yin wannan wa’azi a kai tsaye ko kuma in ba’a iya isa gareshi to ta hannun wanda aka ga zai iya isa. Misali, idan wani shugaba ko attajiri ko wani malami yana yin ɓarna to tilas ne a gyara masa. Idan kuma an ga za’a ba wani shugabanci ko wata amana amma an tabbatar yana da wani aibin da Shari’ah bata so, to wajibi ne a sanar domin in mai gyarawa ne to ya gyara idan kuma ba mai gyarawa bane, to a sanya wanda ake ganin zai iya yin aikin kamar yadda Allah Ya ce. A tuna cewa Abu Sa’id al-Khudri ya ce, Manzon Allah (SAW) yana cewa:-

*“Idan kun ga ana ɓarna to ku kauda ta da hannun ku (watau karfin iko na shuagabanci). Ko kuma ku kauda ta da harshen ku (watau bada shawara ko wa’azi ga wanda ba shi da karfin iko). Ko ku ƙi abin a zuciyarku (watau wadanda basu da dayan biyun da aka ambata)”* (Muslim, hadisi na 16) .

Sai dai wajen yin wa’azi ko bada shawara, tilas ne a yi amfani da hikima da lafazi mai taushi kuma mai kyau kamar yadda Allah Ya yi umurni:-

ٱدۡعُ إِلَىٰ سَبِيلِ رَبِّكَ بِٱلۡحِكۡمَةِ وَٱلۡمَوۡعِظَةِ ٱلۡحَسَنَةِۖ

*Ka yi kira zuwa ga hanyar Allah da hikima da wa'azi mai kyau* (An Nahl:125)

Idan ba'a yi amfani da hikima da lafazi mai taushi kuma mai kyau ba, to, sai Shaidan ya shiga cikin al-amarin ya ƙara dagulashi. Misali, idan wani shugaba yana ɓarna, kamata ya yi a fuskance shi da ladabi ba da zage-zage ko kakkausan harshe ba. A tuna komin ɓarnar shugaba ba zai kai Fir'auna ba, wanda Al-Qur'ani ya bayyana ɓarnarsa:

فَقَالَ أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ

*Sai ya ce, ni ne ubangijinku mafu girma* (An Nazi'at:24)

Ya 'yan-uwana, mu kuma tuna cewa komin wa'azin mutum ba zai kai wani Annabi ba. Duk da hakanan lokacin da Allah Ya aiki Annabawa guda biyu, watau Annabi Musa (AS) da Annabi Haruna (AS), zuwa wajen Fir'auna cewa Ya yi:-

ٱذۡهَبَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ﴿٤٣﴾ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ ﴿٤٤﴾

*Ku tafi (ku biyu) zuwa ga Fir'auna. Lalle shi ya ƙetare haddi (girman kai). Sai ku gaya masa magana mai laushi ko yana tunawa ko kuwa ya ji tsoro* (Ta Ha: 43-44).

Allah (SWT) Ya san Fir’auna ba zai tuna ba kuma ba zai ji tsoro ba, a’a Allah Ya nuna yadda mai wa’azi zai yi wa’azi ne ko da waɗanda zai ma wa’azin manyan masu barna ne.

**Kaicon ka Mai Hassada!**

Ya ‘yan-uwana, babban munin hassada shine mutum, abin halitta, ya riƙa tuhumar Mahaliccin sa, watau Allah (SWT), wai don me ya ba wani ko wata ni’ima daga cikin ni’imominsa waɗanda basu da iyaka? Kai ɗan-Adam, ka yi tunani, shin kai wane ne da zaka tuhumci Mahaliccinka kuma Mahallicin magabatanka da wadanda zasu zo bayanka? Shine kuma Mahallicin sammai da kassai da duk abinda ke cikinsu. Shin ba za ka hankalta ba? Mai hassada dai kullum a cikin bakin ciki yake kuma yana fama da yin gulma, zunɗe, karya, munafunci da dai sauran munanan dabi’u da ayyuka domin ya gudanar da hassadarsa.

Komi yana da asali, kuma asalin hassada dai daga la’antacce Shaiɗan take. Shugaban masu hassada, watau Shaiɗan abin tsine ma wa, shi ya fara yi ma Annabi Adam (AS) hassada domin Allah Ya halicci Annabi Adam a sifa mafi kyautatuwa kamar yadda Allah (SWT) Ya ke cewa:-

لَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَـٰنَ فِىٓ أَحْسَنِ تَقْوِيمٍ

*Ba shakka mun halicci Mutum a cikin mafi kyawon dai-daito ( tsayuwa).* (At-Tin: 4).

Kuma lokacin da Allah (SWT) Ya halicci Annabi Adam (AS) sai Ya umurci Mala'iku su yi masa sujada sai Shaiɗan (wanda ba Mala'ika bane amma yana tare da Mala'iku) ya ƙi yin sujadar kamar yadda Allah Ya bayyana a cikin Al-Qur'ani:-

وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ وَٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ

*Kuma a lokacin da muka ce ga Mala'iku, "Ku yi sujada ga Adam" sai suka yi sujada face Ibilisa ya ƙi, kuma ya yi girman kai, kuma ya kasance daga kafirai.* (Al-Baqara: 34)

Sannan domin rashin kunya da rashin ladabi irin na masu hassada sai Shaiɗan ya kada baki ya kalailaice cewa shi halittarsa ta fi ta Annabi Adamu (AS). Kai, in ban da mai hassada, yaya Allah zai maka ni'imar Magana da Shi har ka kada baki ka nuna hassadarka a fili? Dubi abinda Allah (SWT) Ya ce da amsar da Shaiɗan ya mayar:-

قَالَ مَا مَنَعَكَ أَلَّا تَسْجُدَ إِذْ أَمَرْتُكَ قَالَ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِى مِن نَّارٍ وَخَلَقْتَهُۥ مِن طِينٍ

*(Allah) Ya ce, "Mene ne ya hana ka yin sujada lokacin da Na umurce ka?" (Shaidan) ya ce, "ni ne mafifici daga gare shi (Adam), Ka halitta ni daga wuta alhali kuwa Ka halitta shi daga laka".* (Suratul A'araf: 12)

Shaiɗan bai bar hassadarsa ba sai da ya rubbaci Annabi Adam (AS) da matarsa Hawwa'u (AS) suka kusanci itaciyar da Allah Ya haramta masu a inda suke zaune a cikin Aljanna. Wannan ya sanya Allah (SWT) Ya sauko da Annabi Adam da matarsa Hawwa'u zuwa Duniyar mu. (Al-Baqara: 35-39)

Ya ku yan-uwa Musulmi, ku dubi wannan aya daga Allah. Ashe mai yin hassada koyi yake da Shaiɗan. Burinsa ya raba wanda Allah Ya ni'imta da ni'imar da Allah Ya yi masa. Don haka sai mu yi taka tsan-tsan da mai hassada, shi kuma ya je ya yi ta yi, da sanin cewa makomarsu daya da shugabansu, watau Shaiɗan.

Hassada ce ta sanya Shaidan ya rubbaci ɗan Annabi Adam (AS), watau Kabila har ya cusa masa hassadar ɗan-Uwansa, watau Habila, har ta kai ga shi Kabila ya kashe Habila.

Allah (SWT) Ya bayyana hassadar kafirai ga Annabi Muhammadu (SAW) kamar haka:-

بِئْسَمَا ٱشْتَرَوْا۟ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمْ أَن يَكْفُرُوا۟ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بَغْيًا أَن يُنَزِّلَ

ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۖ فَبَآءُو بِغَضَبٍ عَلَىٰ

غَضَبٍ ۚ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ مُّهِينٌ

*Tir da abin da suka fanshi kawunansu da shi suka kafirce da abinda Allah Ya saukar don* ***hassadar*** *Allah Ya saukar da falalarsa ga wanda ya so daga bayinsa. Sai suka dawo da fushi bisa fushi. Azaba ta wulakanci ta tabbata ga kafirai.* (Al-Baqara: 90)

Kafirai na hassadar Allah Ya saukar da falalarsa ga Annabi Muhammadu (SAW) kuma azabar wulakanci ita ce sakamakonsu. Mai hassada sai ka shirya, domin ba shakka za ka bi sahun ‘yan-uwanka waɗanda zasu gamu da azaba ta wulakanci!

Bayan Allah ya yi bayanin hassadar da kafirai suke yi ma Manzon Allah (SAW) sai kuma Ya yi bayanin hassadar da kafirai ke yi ma Musulmi kamar haka:-

وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا
مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْحَقُّ ۖ

*Da yawa daga Ma’abota Littafi suna burin su maida ku kafirai bayan kunyi imani don* ***hassada*** *daga wurinsu bayan kuwa gaskiya ta bayyana a gare su….* (Al-Baqara:109)

To mai hassada, bayan ‘yan-uwanka sun yi ma Manzon Allah (SAW) hassada sai suka koma ga sauran Musulmi kamar yadda ka ke yi a yanzu.

Hassada dai ita ce tsanin takawa a fita daga Musulunci kuma ita ke hana wanda ba Musulmi ba ya shiga cikin Musulunci. Wannan ya tabbata daga kalmar Allah inda Yake cewa:-

إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلْإِسْلَٰمُ ۗ وَمَا ٱخْتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ
بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۗ وَمَن يَكْفُرْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ
سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ

*Hakikanin Addini wurin Allah shine Musulunci. Waɗanda aka saukar wa Littafi basu yi sabani ba, sai bayan hakika ta zo masu, domin* ***hassada*** *a tsakanin su, kuma wanda ya musanta ayoyin Allah, to hakika Allah mai gaggawar sakamako ne.* (Ali-Imran: 19)

Mai hassada dai ba da wani yake fada ba da Allah Mahaliccin kome da kowa yake yi, domin Allah ne ke bayar da abinda ake hassadar a kansa. Shin, kai ɗan Adam har ka isa ka ce don me Allah Ya ba wani wata falala? Don me zaka rika hushi da zunɗe da baƙin ciki da ƙarya da munafunci akan wanda Allah Ya yi ma wata baiwa?

Ya mai hassada, shin kana da amsar tambayar da Allah (SWT) Ya yi maka kamar haka:-

أَمْ يَحْسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۖ

*Ko kuwa suna yi ma mutane **hassada** ne bisa ga abinda Allah Ya basu daga falalarsa? (An-Nisaa: 54)*

Lallai Allah Mai Rahama ne. Ya ba masu hassada hanyar kubuta da Ya faɗa masu cewa su bar kallo suna hassadar ni'imomin da Ya yi ma wasu daga cikinsu. Wannan ita ce hanya mafi alfanu a gare su. Ko yaushe Allah Ya faɗi aibin wani abu to, zai faɗi hukuncin shi kuma zai faɗi yadda za'a guje masa domin kada a haɗu da azabarsa a lahira. Zaɓi kuma ya rage ga bil-Adama da ya kiyaye ko kada ya kiyaye.

Manzon Allah (SAW) ya nuna cewa abinda ya fi tsoro ga Musulmi ba shirka bane, a'a hassada ce. Uqba bin Amr (RA) yana cewa:-

*Manzon Allah (SAW) ya fito ya yi ma Shahidan Uhud Sallah sai ya wuce zuwa mumbari ya ce, "Ni ne magabacinku kuma mai shaida a kan ku, yanzu ina kallon dausayina mai daraja, kuma ba shakka ina da mabudin duk alhairan da ke Duniya. Na rantse da Allah, bana tsoron zaku yi shirka amma ina tsoron zaku yi **hassada** da juna kuma ku yaki juna saboda abubuwan Duniya"* (Sahih Al-Bukhari kashi na 4, hadisi na 795)

Subhanal-Lah! Saida Annabi (SAW) ya yi rantsuwa da Allah domin ya nuna munin hassada. Manzon Allah

(SAW) ya tabbatar mana da cewa hassada ita ce ke aske addinin mutum ta fitar da shi daga Musulunci. Az-Zubair (RA) yana cewa:-

*Manzon Allah (SAW) ya ce, "Cutar da ta addabi mutanen da suka zo kamin ku, watau* ***hassada*** *da rashin son juna, ta shigo cikin ku. Ban ce cutar zata aske gashin ku ba, a'a, zata aske maku addinin ku ne"* (Al-Tirmidhi, hadisi na 1304)

Kamar yadda Allah (SWT) Ya ke bayar da mafita ga masu laifi, to hakama Manzonsa (SAW) yake yi. Manzon Allah (SAW) ya gargadi Musulmi kamar haka:-

*"Ku yi hankali da zargin juna domin zargi shine zancen karya mafi muni, kada ku yi ta neman laifin wasu kuma kada ku yi leken asirin juna, kuma kada ku yi* ***hassadar*** *juna, kuma kada ku yanke hudda da juna (fiye da kwana ukku), kuma kada ku bar son juna. Ya ku bayin Allah, ku zama 'yan-uwa kamar yadda Allah Ya hore ku"* (daga Abu Huraira (RA), a cikin Al-Bukhari kashi na 8 hadisi na 90)

Ya kai mai hassada, da zargi da bincike-binciken kurakurai ko laifuffukan wadansu, shin baka yarda da abinda Allah Ya horeka bane ko kuma abinda Manzonsa ya hana ka ba? Shin ka taɓa yin tunanin kaima mai kuskure ne kuma mai laifi ne, kila ma fiye da wanda kake zargi? To, ga sakamakon aikin hassada da kake yi:-

Abu Huraira (RA) ya ce Manzon Allah (SAW) yana cewa, *"A hir da **hassada**, ku kiyaye ta, domin ita **hassada** tana cinye kyawawan ayyuka kamar yadda wuta take cinye busash-shin itace*" (Abu Dawud ya ruwaito).

Ya kai mai hassada, Allah (SWT) Ya horeka kuma Manzon Allah (SAW) ya horeka kuma Sahabbai da Manyan Malamai ma basu bar ka ba. Ga kadan daga cikin abinda suka ce:-

Ya zo a cikin littafin "Tanbeehul Gaafileena" na Nasru bin Muhammad as-Samrakandi cewa, *"Babu wani sharri cikin sharrori mafi saurin zartuwa kamar **hassada**, domin kuwa abubuwa guda biyar na nau'in azaba su kan sadu da mai hassada kafin su sadu da wanda ake ma hassadar:-*

1. *Baƙin ciki, da baya yankewa*
2. *Musiba, wacce babu ladar Allah a kanta*
3. *Zargi, wanda babu wani abin yabo tare da shi*
4. *Allah (SWT) Yana fushi da shi*
5. *Za'a rufe mashi dukkan ƙofofin dacewa akan lamurransa".*

Usman bin Hassan Al-Khuri ya faɗa a cikin littafinsa mai suna "Durratun-Nasihina" cewa, Abul-Laisi ya ce, *"Mutum ukku ba'a karɓar addu'arsu;- (1) Maciyin haramun (2) Mai yawan yi da mutane (3) Wanda ya kasance a cikin zuciyarsa akwai hassada"*

Ya zo a cikin littafin “Khamsuna Faredha” na Muhammad bin Abibakr bin Ali, cewa wani daga cikin Manyan Malamai ya ce, *“Ya isar maka daga sharrin mai hassada cewa shi yana cikin baƙin ciki a lokacin da wanda yake yi ma hassadar yake cikin farin ciki”.*

Ya mai hassada, ina fatar wadannan bayanai sun ishe ka sake tunani a kan wannan mummunar ɗabi’a taka. Manzon Allah (SAW) ya baka mafita kamar haka:-

*“Wanda duk ya zalunci wani ta wajen ɓata masa suna ko ta wata hanya daban, to ya je ya roƙe shi gafara kamin Ranar Tashin Kiyama lokacin da babu kuɗin da mai zaluncin zai fanshi kansa da su sai dai idan yana da kyawawan ayyuka to sai a rika ɗibarsu ana ba wanda aka zalunta ko kuma idan babu kyawawan ayyuka sai a rika ɗibar zunubban wanda aka zalunta ana azawa azzalumin”.* (daga Abu Huraira a cikin Al-Bukhari kashi na 3 hadisi na 629).

**Hassada ga Mai Rabo...**

Hausawa na cewa, “Hassada ga Mai Rabo taki ce” watau ana yi maka hassada amma ni’imar da Allah Ya baka tana ta tohuwa kamar yadda shukar da ta ji taki ke toho. Burin mai hassada dai shine ya raba wanda Allah Ya ni’imta da ni’imar da Allah Ya yi masa. Don haka sai a yi taka tsan-tsan da shi, shi kuma ya je ya yi ta yi da sanin cewa makomarsu daya da shugabansu, watau Shaiɗan.

Ya kai wanda ake yi ma hassada, kwantar da hankalinka, kuma kada ka biye ma masu hassadar har kai ma ka shiga cikin ɓarna. Yi hakuri ka kuma tuna ba da kai ake faɗan ba. A'a da Allah (SWT) wanda Ya yi maka ni'ima ko ya baka wata baiwa ake yi.

Ka tuna tun kana ɗan karami aka koya maka karatun Al-Qur'ani inda aka fara da Suratul Fatiha mai koya maka godiya ga Allah da rokonsa falala ta bin hanya madaidaiciya. Surar da ta biyo bayanta wajen koyarwa ita ce Suratul Nas wadda ke koya maka neman tsari daga Shaiɗan. Sura ta ukku ita ce mai koya maka neman tsari daga masu hassada, masu tsafi da sauran halittu miyagu. Wannan ya isa a gane girman sharrin Shaiɗan da masu hassada!

Ya wanda ake yi ma hassada, ka tuna cewa duk wanda Allah Ya ba ilmi, mulki, dukiya da makamantansu, kuma yana amfani da su ta hanyar da Allah Ya ce, to tilas ne miyagun mutane su yi masa hassada.

To, ashe wajibi ne ga wanda Allah Ya daukaka da wata ni'ima ya yi taka tsan-tsan da mahassada. Shi dai ya yi ta yin amfani da ni'imarsa kamar yadda Allah (SWT) ya shimfiɗa. Kuma ya tuna anyi ma Annabawa da Manzannin Allah hassada, tun daga Annabi Adam (AS) zuwa Annabi Muhammadu (SAW). Sahabbai (RA), da Tabi'ai da Tabi'i-Tabi'ina wadanda Manzon Allah (SAW) ya hore

mu da muyi koyi dasu, suma basu tsira daga mahassada ba.

Shehunan Malamai, manyan Sarakuna da sauran Shugabanni, da masu arziki da duk sauran waɗanda Allah Ya ni'imta duk anyi masu ko kuma ana yi masu hassada. Muddin dai Allah (SWT) Ya yi maka wata baiwa kuma kana amfani da ita ta hanya mai kyau, to tilas ne Iblis da shaiɗanun mutane su yi maka hassada. Ka gode ma Allah cewa Ya yi maka ni'ima kuma kana aikin kwarai da ita, domin da kana ɓarna ne, to abin dariya zaka zama ba abin hassada ba.

An samo daga shafi na 20, hadisi na 157, na littafin "Mukhtaril Ahadithil Nabawiyyah" na Sayyadi Muhammad Hashimiy cewa Abu Na'im ya ce, Manzon Allah (SAW) yana cewa:-

*…. Dukkan ma'abocin ni'ima, abin yi ma hassada ne*

**Haza Wassalam,**

Ya kai wanda ake yi ma hassada, kada ka sake mahassada su gane ka yi fushi domin wannan ne zai sa su yi farin ciki. Yi banza da su kamar babu wani abin da ya dame ka, su tai su mutu da baƙin-cikinsu kamar yadda Allah (SWT) Ya umurce ka da yi. Duba Suratu Ali Imran aya ta 119 da ta 120 domin ka samu kwanciyar hankali:-

هَٰٓأَنتُمْ أُوْلَآءِ تُحِبُّونَهُمْ وَلَا يُحِبُّونَكُمْ وَتُؤْمِنُونَ بِٱلْكِتَٰبِ كُلِّهِۦ
وَإِذَا لَقُوكُمْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوْاْ عَضُّواْ عَلَيْكُمُ ٱلْأَنَامِلَ مِنَ ٱلْغَيْظِ ۚ قُلْ
مُوتُواْ بِغَيْظِكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿١١٩﴾ إِن تَمْسَسْكُمْ حَسَنَةٌ
تَسُؤْهُمْ وَإِن تُصِبْكُمْ سَيِّئَةٌ يَفْرَحُواْ بِهَا ۖ وَإِن تَصْبِرُواْ وَتَتَّقُواْ لَا
يَضُرُّكُمْ كَيْدُهُمْ شَيْـًٔا ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعْمَلُونَ مُحِيطٌ ﴿١٢٠﴾

*Ku ya waɗannan, kuna son su amma basu son ku, kuma kun yi imani da Littafi (Qur'an) dukkansa. Kuma idan sun haɗu da ku sukan ce, "mun yi imani". Amma idan sun kadaita sai su ciji yatsu a kan ku domin takaici. Ka ce masu "ku mutu da takaicin ku". Lallai Allah Masani ne ga abin da ke cikin zukata. Idan wani alheri ya shafe ku sai ya bakanta masu rai kuma idan wata cuta ta shafe ku, sai su yi farin ciki da ita. Kuma idan kuka yi hakuri, kuma kuka yi takawa, kaidinsu baya cutar ku da kome. Lallai ne, Allah mai kiyayewa ne daga abinda suke aikatawa".*

Ya wanda ake yi ma hassada, kai dai ita yin kyawawan ayyuka kuma ka yi ta yin addu'a Allah Ya kare ka daga sharrin mahassada kamar yadda Ya ce kayi:-

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلْفَلَقِ ﴿١﴾ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ﴿٢﴾ وَمِن شَرِّ غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ
﴿٣﴾ وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِى ٱلْعُقَدِ ﴿٤﴾ وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ﴿٥﴾

*Ka ce, "ina neman tsari ga Ubangijin safiya. Daga sharrin abin da Ya halitta. Kuma daga sharrin dare idan ya yi duhu. Kuma daga sharrin masu tofi a cikin kulle-kulle. Kuma daga sharrin mai hassada idan ya yi hassada".* (Al-Falaq: 1-5)

Sayidatuna Aisha (RA) tace:-

*Duk lokacin da Manzon Allah (SAW) ba shi da lafiya, Mala'ika Jibreel yana karanta wannan addu'a:- "Da sunan Allah, Zai warkar da kai daga wannan ciwo kuma Ya kare ka daga sharrin mai hassada lokacin da ya yi hassadar da kuma sharrin masu kandun idanu"* (Muslim, hadisi na 1026).

Ya kai mai hassada, ga irin azabar da Allah (SWT) Ya tanadar maka:-

وَيْلٌ لِّكُلِّ هُمَزَةٍ لُّمَزَةٍ

*Bone (azaba) ta tabbata ga mai nune, mai zunɗe (mai rada domin hassada)* (Hummaza: 1)

Malamai sun yi amafani da hadissan Manzon Allah (SAW) suka yi ittifaƙi da cewa "Wailun" na nufin wani rami mai zurfi a ƙarƙashin wutar Jahannama inda za'a yi ma manya-manyan masu laifi azaba kamar su Fir'auna da masu hassada.

Allah (SWT) Ya kuma tanadar ma masu hassada, musamman masu yawo suna watsa labaran barna ga masu imani, azaba a duniya da lahira, a inda Ya ke cewa:-

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحِبُّونَ أَن تَشِيعَ ٱلْفَٰحِشَةُ فِى ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ
فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ ۚ

*Lallai ne waɗanda ke son watsa alfasha ga waɗanda suka yi imani, suna da azaba mai radadi a cikin duniya da lahira.* (Nur:19)

Ya kai mai hassada, Allah (SWT) mai karbar tuba ne don haka ya kamata ka tuba ka bari, kamar yadda Allah Ya ce a Suratul Hujurat aya ta 12:-

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱجْتَنِبُوا۟ كَثِيرًا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعْضَ ٱلظَّنِّ إِثْمٌ ۖ
وَلَا تَجَسَّسُوا۟ وَلَا يَغْتَب بَّعْضُكُم بَعْضًا ۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمْ أَن يَأْكُلَ لَحْمَ
أَخِيهِ مَيْتًا فَكَرِهْتُمُوهُ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ تَوَّابٌ رَّحِيمٌ

*Ya ku wadanda suka yi imani. Ku nisanci abu mai yawa na zato. Lallai sashen zato, laifi ne. Kuma kada ku yi tone-tone, kuma kada sashenku ya yi gibar sashe. Shin ɗayanku na son ya ci naman ɗan-uwansa matacce? To, sai kuka ki cin shi. Ku bi Allah da taƙawa, lallai Allah mai karɓar tuba ne mai jin ƙai.*

Daga ƙarshe, ina kira ga mai hassada da ka tuba ka bari kamin Allah (SWT) Ya kauda ka daga Duniya zuwa inda babu tuba kuma babu abin fansar kai. Sai dai a riƙa ɗibar ladar ka ana ba waɗanda ka zalunta. Idan kuma babu ladar, sai a riƙa ɗibar zunubban waɗanda ka zalunta ana labta maka. Wal-iyazu-bil-Lah!

*Wassalamu Alaikum*

**Prof. Sani Abubakar Lugga, MFR**
**Wazirin Katsina**